Ban tava yin ciwon kai ba ko ciwon Ido tunda Manzon Allah SAW ya shafi fuskata, kuma yayi mun tofi a idona a ranar Khaibar lokacin da ya bani Tuta

Daga Aliyu Bn Abi Xalib -Allah ya yarda da shi- ya ce: "Ban tava yin ciwon kai ba ko ciwon Ido tunda Manzon Allah SAW ya shafi fuskata, kuma yayi mun tofi a idona a ranar Khaibar lokacin da ya bani Tuta"

[Hasan ne] [Abu Ya'ala ya Rawaito shi - Ahmad ne ya rawaito shi]

Aliyu Bn Abi Xalib ya kasance yana fama da Ciwo a Idanuwansa, saboda toka da ta shigar masa a yaqin Khaibar, sai Manzon Allah SAW sai ya shafi fuskarsa kuma yayi tofi a cikin Idanunsa sai ya warke da yardar Allah sannan ya bashi tuta, kuma Allah ya bashi Nasarar buxe ganuwar Khaibar, kuma Ali -Allah ya yarda da shi- cewa shi Ban tava yin ciwon kai ba ko ciwon Ido tunda Manzon Allah SAW ya shafi fuskata, kuma yayi mun tofi a idona a ranar Khaibar lokacin da ya bani Tuta

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/10956